FICHE PRATIQUE

# Shin ƙungiyar ku na cika waɗannan mafi ƙarancin ka'idoji na korafe-korafe da karɓar ra'ayoyi?

Muhimman ka'idoji

## TSARIN

| Kungiyar nada wani tsarin gudanar da korafe-korafe da karɓar ra'ayoyi | | EH | A'A |
|---|---|---|---|
| 1 | Direktar/Shugaban zai tabbatar an rubuta ka'idar korafe-korafe da karɓar ra'ayoyi, wanda wani masanin fasaha zai duba, da mashawarta (inda ya dace) sannan a amince dashi bisa ga ka'idoji na duniya. | | |
| 2 | Direktar zai tabbatar cewa akwai hanyoyi masu aminci, wanda kowa na iya samu kuma mai sirri a cikin ka'idar don bayanai sirri (magudi, amfani da dama da cin zarafi ta fuskar jima'i) | | |
| 3 | Kayayyakin da ake buƙata don kafawa, aiki da lura da tsarin an haɗa tare da kasafin kuɗi, ko an haɗa a cikin takardun neman kuɗi na gaba. | | |
| 4 | An zaɓa matsayin gudanar da korafe-korafe kuma an sanarwa ma'aikatan shirin. | | |
| 5 | An yi bitar ka'idar korafe-korafe da karɓar ra'ayoyi a hukumance bisa ga bayanin da aka samu daga al'ummomin da abun ya shafa da kuma bincike akan yadda yake aiki a wani jerin lokaci na aiwatarwa. | | |
| **An fifita tsaron wanda ya kawo korafin da waɗanda abun ya shafa a dukkan matakai. (CHS)** | | **EH** | **A'A** |
| 6 | An gabatar da wajibai buƙatun rahoto na ƙungiyar da ƙungiya mai jagora ga dukkan ma'aikata | | |
| 7 | Ma'aikata sun fahimci yadda zasu tura zargin saba dokokin aiki kuma an sake tura waɗannan zuwa hukumar da ya dace a cikin awanni 24. | | |
| 8 | Ya kamata ma'aikatan da aka yiwa horo wanda suka sadaukar da kansu ne kawai zasu tallafawa zargin amfani da dama da cin zarafi ta fuskar jima'i (PSEA), da lura cewa akwai buƙatar rage yawan ma'aikata "da aka zaɓa musamman" wanda za'a turawa bayanai sirri. | | |

## MAGANCE KORAFE-KORAFE

| | Ana marabtar kuma ana amince da korafe-korafe da ra'ayoyin jama'a, kuma an sanar akan yadda za'a samu damar tsarin da kuma yawan matsalolin da za'a iya magance. (CHS) | EH | A'A |
|---|---|---|---|
| 9 | An horar da ma'aikata akan ka'idodin ɗaukan alhaki da kuma tsarin karɓar korafe-korafe da ra'ayoyi na ƙungiyar. | | |
| 10 | Ya kamata dukkan ma'aikata su samu ka'idar gudanar da korafe-korafe da karɓar ra'ayoyi, hadda kowane sigar da aka sabunta. | | |
| 11 | Ana bada bayani akai-akai akan haƙƙin yin korafi da bada ra'ayi, ta yaya kuma a ina zuwa masu ruwa da tsaki da al'ummomi. Wannan zai iya zama ta taron musayar bayanai, a lokacin gudanar da ayyukan shirin, fosta, ƙananan takardun talla. | | |
| 12 | Ana bada bayani akan ka'idodin ƙungiyar ku na halin da ya kamata a wajen aiki zuwa masu ruwa da tsaki. | | |
| 13 | An samar da bayanin a harsunan yanayin da ya dace, tsari da hanyar don tabbatar mata, maza, yara, mutane masu nakasa, da mutanen da basu yi karatu na iya samu | | |
| 14 | An kula da abubuwan da al'umma ke tsammani ta sadarwa a bayyane akan irin bayanai da ake amince dasu (na sirri da/ko wanda ba na sirri) | | |
| 15 | An kula da abubuwan da al'umma ke tsammani ta sadarwa a bayyane akan irin bayanai da ake amince dasu (na sirri da/ko wanda ba na sirri) | | |
| | **Ana gudanar da korafe-korafe akan lokaci, kuma ta hanyar da ya dace mai adalci. (CHS)** | **EH** | **A'A** |
| 16 | An zaɓi ma'aikata musamman masu aiki wanda akwai shaidar nuna gaskiya, rashin son kai, iya lura da sirri da kwarewa wajen sadarwa da al'ummomi daban-daban don magance korafe-korafe da ra'ayoyin jama'a. | | |
| 17 | An tattauna tare da masu ruwa da tsaki kafin tsara CFRM; kuma an zaɓa kuma an tsara hanyoyin samun dama guda biyu don bari a samu dama mai ma'ana cikin sirri sakamakon tattaunawar. | | |
| 18 | An horar da ma'aikata akan yadda zasu taimakawa mutane don kai rahoton korafi ko wani matsala, ko don bada ra'ayi. | | |
| 19 | An fayyace tsayayyen lokuta da ƙarshen lokaci don amince da rufe korafin. | | |
| 20 | An shirya rahotannin wata-wata akan yawan korafe-korafe/ra'ayoyi da aka samu tare da nazarin irin matsalolin da aka samu da kuma tsawon lokacin da ya ɗauka kafin a magance su. | | |

**FICHE PRATIQUE**

| | **Korafe-korafe da ra'ayoyi da basu shafi ƙungiyar an tura su zuwa hukumar da ya dace bisa ga mafi ƙarancin ka'idodin turawa gaba. (CHS)** | **EH** | **A'A** |
|---|---|---|---|
| 21 | Akwai bayani akan wasu hidimomi da masu bada hidimomi kuma ma'aikata suna samun taswirar hidimomi da tsarurrukan karɓar korafe-korafe da ra'ayoyi da aka sabunta. | | |
| 22 | Ba za'a tura gaba ba tare da neman izinin wanda ya kawo korafin. Tare da Zaɓin wanda ya kawo korafin ya zama a sirrance. | | |
| 23 | Daidai gwargwado a sanar da dukkan wa'yanda suka kawo korafi kuma a musu bayani akan shawarara da aka yanke game da matsalar su. | | |
| 24 | Daidai gwargwardo an sanarwa dukkan masu korafi akan haƙƙin su na daukaka kara | | |

## BAYANAI DA AKA AJIYE DA BAYANAI DA AKA TATTARA

| | **Ajiye bayanai yana bin tsari, kuma ana lura da bayanai da aka ajiye, ana sabunta kuma daidai ne.** | **EH** | **A'A** |
|---|---|---|---|
| 25 | Mafi ƙarancin bayanin da ake buƙata don gudanar da korafin ko don maida amsa ake tattara kawai, kamar yadda aka fayyace a ka'idar. | | |
| 26 | An aiwatar da kowace rabiyar kashi, fifiko da sashi da kowace 'bayani', kamar yadda aka fayyace a ka'idar. | | |
| 27 | An yi nazari akan bayanai mara nuna asalin masu shi, kuma an tattauna akan yanayi ko a bada rahoton shi bayan kowane watanni uku don taimakawa wajen koyon buƙatun masu ruwa da tsaki da sauyin shirin. | | |

## HATSARORI

| | **Ana darajanta sirri, kuma ana tattara, amfani da tsare bayanai kai yadda ya kamata.** | **EH** | **A'A** |
|---|---|---|---|
| 28 | Samun dama da amfani da bayanin wanda ya kawo korafin sai da umurni kawai. An tsare bayanin da kalmar sirri. | | |
| 29 | An fadawa masu korafi ka'idar tsare sirri na ƙungiyar, kuma an tambaye su idan sun bada izinin bayar da bayanin su kuma ko sun fahimci yadda za'a amfani da wancan bayanai. | | |
| 30 | An horar da dukkan ma'aikatan da suke tattara bayanai akan ka'idodin turawa gaba mai aminci da shaida. | | |

Idan ƙungiyar ku basu cika waɗannan mafi ƙarancin ka'idodi da fatan za'a ɗauki mataki don bitar tsarin karɓar korafe-korafe da ra'ayoyi. Idan ƙungiyar ku na buƙatar taimako da fatan za'a tura email zuwa shugaban fannin a yankin ku, da Kungiyar masu jagora da daidaita aiki, lebbeia@unhcr.org



Plus d'outils et de conseils
pour communiquer avec les communautés sur le site : cwc.westafrica.exposed